Na haneku da shiga wurin mata" sai wani mutum daga mutanen Madina ya ce: Ya Manzon Allah, shin kana ganin ƙanin miji fa? ya ce: "Ƙanin miji (shi ne) mutuwa

Daga Uƙubah ɗan Amir - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Na haneku da shiga wurin mata" sai wani mutum daga mutanen Madina ya ce: Ya Manzon Allah, shin kana ganin ƙanin miji fa? ya ce: "Ƙanin miji (shi ne) mutuwa".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya tsoratar daga cakuɗuwa da mata ajanibai (waɗanda ba muharramai ba), ya ce: Ku kiyaye kawunanku da ku shiga gurin mata, mata kuma su shiga gurinku. Sai wani mutum daga mutanen Madina ya ce: Shin kana ganin makusantan miji fa; kamar ɗan uwan miji da ɗan ɗan uwansa, da baffansa da ɗan baffansa, da ɗan 'yar uwarsa, da makamancinsu daga waɗanda aure da su yake halatta gare shi da a ce ba mai aure ba ce? Sai (Annabi) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: Ku kiyaye shi kamar yadda kuke kiyayar mutuwa! domin kaɗaitaka da 'yan uwan miji mai kaiwa ne zuwa ga fitina da halaka a cikin Addini, makusantan miji banda iyayensa da 'ya'yansa sune mafi cancanta da hani cikin ajnabi; domin kaɗaitaka da makusancin miji tafi yawa daga kaɗaitaka da waninsa, kuma sharri ana tinanin afkuwarsa ne daga gare shi sama da waninsa ba tare da wani inakri akansa ba, kuma domin cewa shi babu makawa daga gare shi , kuma tsare shi ba ya yiwuwa daga gareta, yayin da al'ada ta gudana da sassauci a cikinsa sai namiji ya keɓanta da matar dan uwansa; to shi yana kama da mutuwa a muni da barna, sabanin namiji ajnabi cewa shi ana kulawa daga gare shi.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/5888